# HAUSA FULANI A IDON NA KUSA DA NA NESA

Muhammad Abubakar Zabi
Jami'ar Usmanu [Anfodiyo, Sakkwato
muhammadabubakarzabi@gmail.com

Shamsuddeen Isma'il
Shehu Shagari College of Education

***TSAKURE***

*Fulani da Hausawa al'umma ce da]]iya wadda ban da Allah ba wanda ya san lokacin ha]uwarsu, sakamakon }arancin kayan rubutu a wancan lokacin. Fulani na cikin }abilu na farko-farko da Hausawa suka fara cu]anya da su. Wannan shi ya kawo bazuwar Fulani ko'ina cikin} asar Hausa. Shi ya sanya wasu makwabtansu na nesa ke yi musu kallon abu guda kawai. Haka kuma shi ya samar musu da sunan Hausa-Fulani sakamakon daddediyar mu'amala wace ta saka suka caku]a da juna, wanda yanzu an kai fagen da Bafulatani ko Bahaushe ba zai iya tantance cewa shi kaza ne, saboda an yi auratayya an kuma gauraya waje guda. Wanda zai yi wuya ka }irga kaka biyu ko uku na zuriyarku baka tarar da wani sirki na Bahaushe ko Bafulatani ba. Ko ta wajen Uwa ko ta wajen Uba. Wannan aikin sai waiwaici asalin Fulani a takaice da na Hausawa da zamatakewa da suturar Fulani da kuma suturar Hausawa. A takaice wannan takarda za taduba yadda ake kallon Hausa Fulani a idon nakusa da na nesa.*

## GABATARWA

Hausawa da Fulani, wasu al'umma ce da Allah ka]ai ya san irin ajiyar da ya yi. Ku san za a iya cewa ha]in Allah ne, wanda duk yace zai raba Hausawa da Fulani to! Tamkar zai iya raba hanta da jinni ne. Dangatakar zamantakewar Hausawa da Fulani mahdi ne mai dogon zamani. Abu ne mawuyaci a iya gano lokacin da Hausawa da fulani suka fara hul]a. Amma a ruwayar Maigandi Attahiru(2003) masana irinsu Malam Abdullahi Gwandu da Waziri Sakkwato da suka yi fa]i tashin gane hakansun yi kirdadon gano cewa, Fulani na cikin }abilu na farko-farko da Hausawa suka fara cu]anya da su. Wannan shi ya kawo bazuwar Fulani ko'ina cikin }asar Hausa. Shi ya sanya wasu makwabtansu na nesa ke yi musu kallon abu guda kawai, kamar Iyamurai da Yarbawa da sauransu }abilu na nesa. Haka kuma shi ya samar musu da sunan Hausa-Fulani sakamakon da]]e]iyar mu'amala wace ta saka suka caku]a da juna, wanda yanzu an kai fagen da Bafulatani ko Bahaushe ba zai iya tantace cewa shi kaza ne, saboda an yi auratayya an kuma gauraya waje guda. Wanda zai yi wuya ka }irga kaka biyu ko uku na zuriyarku baka tarar da wani sirki na Bahaushe ko Bafulatani ba.Ko ta wajen Uwa ko ta wajen Uba.

## WAIWAYE

Funtua (2010) ya gabatar da mu}ala mai taken Tufafin Hausawa da Fulani na gargajiya. Bayan ya kawo gabatarwa sai ya kawo ire-iren tufafin Hausawa na gargajiya. Yanda ya yi bayanin tufafin maza da mata, da kuma tufafin da ba}i suka kawo.

Shi kuma [anmaigoro, (2010). Ya gabatar da takardarsa mai taken Magungunan Hausawa da Fulani. Bayan ya kawo gabatarwa sai ya duba Bokanci da Bori da Maita da Tsibbu da Magori da Ungozoma. Sannan sai ya duba Magungunan sana'o'i, yanda ya duba Wanzamai da Ma}era da Mahauta da Masunta da kuma Ma]ora. Daga }arshe kuma ya kawo muhimmancin magungunan gargajiya ga Hausawa da Fulani.

Busa da Isa (2015) sun gabatar ta takardarsu mai taken kalmomin Makwabtan }abilu a harshen Hausa. Yanda suka duba mene ne harshen Hausa da kuma Hausawa da makwabtansu, da are-aren kalmomi daga makwabtan Hausawa zuwa harshen Hausa. Sai kuma su ka yi bayani dangane da al'ummar Fulani da kuma kalmominsu da aka ara. Yarbanci da kalmominsu. Da Barebari da kalmominsu da aka ara, da al'ummar Azbinawa da kalmominsu da aka ara, da al'ummar Nufe da kalmominsu da aka ara, da kumaal'ummar Gwari da kalmomin da Hausawa suka ara.

**ASALIN HAUSAWA A TA}AICE**

Manyan masana irinsu farfesa Mahdi Adamu, Hambali Jinju da farfesa M.G Smith da Farfesa Abdullahi Smith da Farfesa Aliyu Muhammad Bunza da sauran manyan masana da dama sun zo da ra'ayoyi mabambanta a Kan asalin Bahaushe. Kamar yadda John paden (1967-1970b) da Abner Cohen (1969). {o}arin tantace zaman mutum Bahausheya danganci cu]anyarsa da waiwalarsa cikin abokan sabga. Kalmar Hausa ta }unshi taron dangi na sassan }abilu barkatai.

A mahangar Mahdi Adamu Bahaushe shi ne:

"Wanda a tarihinsa daga }asar Hausa ya
tsira ko zuriyarsa ta fuskar iyaye maza da,
haka kuma wa]anda suka sha}u da al'adun
Hausawa sosai suka ri}e harshen da ]abi'unsu
da addininsu".

Abdullahi Smith ma cewa ya yi:

"Yana ganin Hausawa da harshensu na da
ala}a ne da harsunan da ake }ira harsunan
chadi wa]anda ake ganin a can da harshe ne
dun}ulalle guda ]aya, amma daga baya kamar
shekaru dubbai da suka wuce suka rarrabu zuwa
harsuna irinsu Angas, Bachama da Bade da Bolanci
da Bura da Hausa da Margi da Miya da kare-kare da Kana
kuru da Mandara da Ngizim da sauransu."

Smith na ikirarin cewa Hausawa mutane da a da can suke zaune a}asar da yanzu ake kira Jahuruyar Nijar. A wancan lzokaci Allah ya albarkaci }asar da Itace, ciyayi da rafuka da }oramu da ban ruwa.

A mahangar Bunza, (2014) cewa ya yicikin yun}uri tantace Bahaushe ya kyautua waiwayi }irar zatinsa, da ]abi'unsa, domin fayyaceBahaushen gado da taho-na-taho da maziyartada makwabta da aka Hausantar a ilmantance. Bahaushen asali za a same shi:

"Yana da ba}i sosai irin na jama'ar tsakiya
sudaniya. Zubin kansa na da tsawo da }urungun

kai mai ]an jemo zai same shi".

Wa]annan sifofi na zati, da launi, idan aka }ura musu idon nazari za a iya fitar da Bahaushe kai tsaye a taron jama'ar da ke zaune a }asarsa. (Bunza 2014). Kamar yadda muka gani cewa masana sun kawo wane ne Bahaushe: Bisa ga yadda masana da manazarta suka ce za mu iya cewa, Bahaushe shi ne, mutumin da yake zaune a }asar Hausa, ta fuskar launi kuma ba}i ne; kuma iyayensa Hausawa ne,idan kuma ba a }asar Hausa yake zaune ba, ya kasance yana jin Hausa, kuma wasu al'adun Hausawa sun yi tasiri a gare shi,to wannan shi ne Bahaushe.

**ASALIN FULANI A TA}AICE**

Masana da suka yi rubutu a kan asalin Fulani sun bayyana shi a zaman mai sar}a}iyakamar na Hausawa. Daga cikin wa]anda suka yi wannan }o}arin sun ha]a da Malam Abdullahi Gwandu }anin Mujaddadi Shehu Usmanu [anfodiyo da Wazirin Gwandu.

Malam Abdullahi A cikin littafinsa, Tazyin al-wara}at cewa, Fulani sun fito ne daga tsatson U}ubatu ]an Nafi'u wanda ya ce Balarabe ne kuma Sahabi Babba. Ya zo }asar Masar inda ya auri ýar Sarkin garin mai suna BujjaMugga sai suka haifi ýaýa hu]u wa]anda su ne asalin Fulani da Fulatanci.

Shi kuma Wazirin Sakkwato Malam Junaidu a littafinsa Tarihin Fulani cewa ya yi Fulani sun ta sone daga Durisininata }asar Sham har suka iso Futa Toro ta }asar Sinigal suka zauna garin har suka yi yawa. Nan ne a cewarsa U}ubatu ya sadu da su har suka shiga addinin musulunci.

{ari ga wannan ra'ayin Waziri Junaidu ya rawaito cewa akwai masu ra'ayi Fulani asalinsu zuriyar Rama ne ]an Annabi Isha}a ]an Annabi Ibrahim (A.S) ya kuma bayyana ta la'akari da wannan ra'ayi cewa, sun taso ne daga futa Toro da nufin komawa }asar Larabawa a }ar}ashin jagorancin wani babban Malami Musa jakollo. Daga cikin zuriyyarsane aka haifi Shehu Usmanu [anfodiyo. Sun zauna a }asar Gobir ana kiransu da suna Torankawa saboda fitowa daga Futo Toro.

Haka kuma bincike ya nuna cewa mazaman farko na Fulani yan yankin }asar Senegal ne na Afirka ta yamma. Daga nan ne sannu a hankali suka ba zu zuwa }asashen chadi da kamaru. A cikin }arni na sha hu]u ne suka shigo }asar Hausa. Dalilin shigowar Fulani }asar Hausa kuwa shi ne, sanadiyar }aura da suke yi daga Senegal zuwa gabashi, domin neman makiyaya mai kyau. A cikin farkon }arni na sha shida akwai al'umomin Fulani masu yawan gaske a }asar Hausa . sannu a hankali kuma a cikin }arni na sha bakwai wasu Fulani da ke zaune }asar Hausa suka yi kudu maso gabas har suka iso kogin Gongola suka mamaye wurin saboda yanayinsa na dausayi da makiyaya mai kyau. Fulani ba su da wata sana'a wadda ta wuce kiwo. A yau al'ummar Fulani sun ha]e da ta Hausawa har ma ana ganinsu a matsayin al'umma ]aya. (Funtua 2010)

Ta la'akari da yadda masana da manazarta suka ce dangane da asalin Fulani za mu iya cewa,asalin Fulani Larabawa ne wanda asalinsu a gabas ta tsakiya suke, kuma suna daga cikin zuriyar Annabi Ibrahim (A.S). Saboda yanayi da kuma }aura-}aura ce na neman abinci da wajen kiwo ya sa Fulani barin wajen su na asali suka zo yadda suke zaune a yanzu.

**ZAMANTAKEWA**

Zamantakewa na nufin kamar yadda sunan ya nuna daga Kalmar zama, wato abin nufi a nan shi ne zaman tare, ya'allah ko dai ta fuskar zumunta ko makwabta, ko kuma ta fuskar yanayin

sana'a, ko da yake ma'anar takan iya wuce wannan idan aka yi la'akari da ire-iren dangantakar da ake samu tsakanin al'umma.

Hausawa sun da]e suna hul]a da }abilun da ke zagaye da su. Wannan kuwa yafaru ne a sanadiyar kasuwanci ko }aurace-}aurace. A cikin gida Nigeriya za a iya kasa zamantakewar Hausawa da sauran }abilu zuwa gida biyu. Gidan farko shi ne Hausawa da sauran }abilu da suke a rewancin Nigeriya. A arewa harshen Hausa ya zama harshen }asa wanda da sauran }abilu ne ke amfani da shi. Idan}abilu uku ko hu]u sun ha]u harshen da suke amfani da shi wanda kowannensuna ji shi ne harshen Hausa. Don haka ma a jamhuriya ta farko aka mai da harshen Hausa ya zama harshen da ake amfani da shi a majlisar dokoki ta kaduna. Hausawa sun bazu ya zuwa sauran garuruwan }abilun arewacin Najeriya irinsu Jos, da Adamawa, da Borno da Bauchi da Kaduna da kuma Niger da sauransu. Haka kuma al'adunsu da suka ha]a da abinci da tufafi da muhalli duka sun sami kar~uwaa jahohin Nigeriya, da wanda ba na Hausa ba.

A ~angaren zamantakewa kuma da makwabtan Hausawa a kudanci da gabashin Najeriya kuwa Hausa na da kyakkyawar ala}ata kasuwanci da su. Da yake zamantakewar Hausawa da }abilun da ke kewaye da su ta bambanta da yadda take da jama'ar kudanci ko gabashi, wannan ne ya sa Hausa caku]uwa da wa]annan al'ummu, sai suka kakkafa unguwanni nasu yasu-yasu. A kudanci Najeriya Hausawa kan kira wa]annan unguwanni da suna "Sabo" Don haka ne suke da sabo-Ibadan, Sabo- ile-ife. A kudancin Najeriya kuwa akwai unguwannin Hausawa irinsu Agana Bodi da sauransu. A sakamakon zamantakewar Hausawa da Fulani, aka samu ala}a ta kusa sosai wanda har ta kai yanzu ba a iya bambance Bahaushe da Bafulatani. Auratayya tsakanin Hausawa da Fulani, Fulani suka wanke Bahaushe ya zama kyakkyawa mai kyan siffa, koma bayan a da Bahaushe baki gajere mai }aton kai.

## KALLO DA NA NESA SUKE YI WA HAUSA-FULANI

Bisa dukkan alamu makwabtan Hausa-Fulani da suke nesa suna yi wa Hausa-Fulani ku san abi guda ne. Amma abin ba haka yake ba, saboda dukwani Bahaushe da ya taho daga Arewa ko Bafulatani, wanda ya yi karatu da wanda bai yi karatu ko ]an kasuwa gani suke duk abu guda ne. Domin su ba sa la'akari da wasu ]abi'u ko halaye ko kuma al'adu da take bambantasu. Babba abin da suke kallo kawai shi ne, ya fito daga Arewa ne,a tunanin mafi yawansu.In dai ba shanu suka ga mutum yana kiwo ba, ko Bafulatana tana tallan nono ba; to kawai Hausa-Fulani ne. Su a kallonsu wanda yake kiwo shi ne Bafulatani, amma duk wanda ya zo da sa~anin haka kawai za su kira shi da Hausa-fulni ne.

## KALLO DA NA KUSA SUKE YI WA HAUSA FULANI

Ga alama kallon da makwabtan Hausawa na kusa, ya sha bamban da kallon da makwabtansu na nesa su ke yi musu. Su makwabta na kusa suna iya bambance Bahaushe da Bafulatani ta hanyar siffa da halaye dakuma wasu al'adunsu. Misali, ta hanyar siffa duk inda ka ga Bafulatani fari neakasari, haka kuma gashinsu a mur]e yake. kuma mafi yawansu sirara ne, dogaye. Haka kuma ba su da sakin jiki, suna da kunya. Amma Bahaushen kwarai za a sami shi ba}ine sosai, kuma zubin kansa na da tsawo da kurungun kai mai ]an jemo. Ta fuskar Gaisuwa, Tafiya da Mu'amula da Auratayya da Mutuwa da Shugabanci da Sana'a da kuma

Tsarin gine-gine, duk wa]annan ]abi'u makwabta Hausa-fulani na iya bambance su ta wa]annan hanyoyi. Kuma zai yi wuya ka ga Bafulatani ya ci maka abinci a kan hanya. Amma Bahaushe ya sha bamban da wannan ]abi'a ta Fulani.

Haka kuma Bafulatanin jeji za ka same shi da malafa da sanda da kuma jallon ruwa, idan kuma saurayi neza ka same shi da madubi dasanda da malafa, da kuma wu}a. Wanda wannan halayya ta sha bamban da ta Bahaushen ko da kuwa na jeji ne ba za ka same shi da wa]annan abubuwa ba. Ta fuskar abincinsu kuwa, makwabtan suna iya bambance su. Ta fuskar abinci kuwa, Bahaushe yana da tuwo da [anwake da Tubani da Dambu da Waina da [anbagalage da {uli-}uli da kwa]o da kuma Da}uwa da sauransu. Sai dai Bafulatani zaka same shi da Fura da nono da Kunun kanwa da Kunun tsamiya da Kwa]on rama da Tanta]i da Sha~e da Kasambara, da sauransu.

Ta ~angaren sunaye ma sun sha bamban da juna, misali Bahaushe zaka ji, Gambo da Juj da jinjiri da Zinaru da Kyauta da Kanta da Ayashe da Talle da Magaji da Korau da kuma Tunau da sauransu. Amma Fulani kuwa zaka ji ana cewa, Haro da Lari da Yi]i da Innayo da Toka da Kaku da Jungu]o da Bello da Shanono daJuli daOri da ýako da kuma Wammi da sauransu. Ta ~angaren furuci kuwa ma}wabtan Hausawa na kusa na iya bambance su. Misali Bafulatani ya kan ce "Zan shi maimakon Zan ci". Haka kuma Bahaushe ba iya fa]in }osan sai dai ya ce Kwasan. Duk wa]annan makwabtan Hausawana kusa suna iya bambance Hausawa da Fulani ta wa]annan hanyoyi da aka lissafa a sama. Koma bayan na nesa.Sabi da ba sa tare da su. Balle su ga wasu ]abi'unsu ko halaye domin su iya bambance waye Bahaushe ko Bafulatani.

A takaice kallon da na nesa ke yi wa Hausawa da Fulani a matsayin abu guda.Ya sa mu ne a sakamakon ba tare da su suke ba a waje guda. Kuma sun tashi sun ga Hausawa da Fulani waje guda, Da rashin sanin waye Bahaushe da Bafulatani, sannan kuma sun lura da kowanensu Hausa yake yi. Haka kuma su a tunaninsu duk wani ]an Arewa Hausa Fulani ne. Haka kuma sun kula da cewa yanayin zamantakewarsu da auratayya tsakaninsu duk guda ne. Kuma suna kishin junansua waje. Don haka ne ma suke cewa Hausa-Fulani. Amma na kusana yi musu kallo ne, irin na mutum da makwabcinsa. Domin tare suka tashi, Kuma za a iya cewa tare aka haife su har suka yi wayo tare. Don haka ne, su kallon da suke yiya sha bamban da wanda na nesa ke yimusu.

## SUTURAR HAUSAWA

Hausawa suna zaune ne a wurare wa]anda ke da jigawa da rairayi. Haka kuma ta wata fuskar akwai daji mai itace masu matsakaicin tsawo da ciyayi da }oramu da rafuka. Saboda haka a lokacin sanyi }asar Hausa tana da tsananin sanyi, kuma alokacin zafi take da tsananin zafi. Wannan shi ne ya sanya galibin tufafin Hausawa suke da yalwa. Haka kuma akwai masu kauri da kuma nauyi matu}a, kumaan fi yin amfani da su a lokacin sanyi. Idan lokacin zafi ne, to akasari tufafin Hausawa basu da nauyi sosai.

Kalmar sutura dai ararriyar kalma ce daga larabci(suturatu) da manufar tufafi da ke rufe wa mutum al'aurarsa, wato dai duk tufafin da ke isar mutum Muslmi ga yin sallah. Amma awajen Bahaushe Kalmar tana da ma'anar tufafi isassu da za su kare mutuncika daga tsiraici da kowanne iri ne, sababbi ne, ko tsofaffi in dai sun kare tsiraici, ana kiransu sutura.

Tufafin Hausawa sun kasu kashi biyu kamar haka:

1- Tufafin gargajiya na Hausawa
2- Tufafi bayan ha]uwarsu da baki

**Tufafin Gargajiya Na Hausawa**

A zamanin da Hausawa suturarsu mafi yawaba ta wuce daga cibiya zuwa guiwa. Domin tun zamanin da Bahaushe yana da kunyar nuna tsirancinsa a waje. Ga misalai kamar haka:

1- Kwarkwaro
2- Bante
3- Kirshe
4- Ganye
5- Rabaja
6- Ya~a
7- Jigida
8- Kanfai/kalimsho
9- Walki

**Bayan Bahaushe Ya Ha]u Da Baki**

Wannan yana nufin lokaci da Bahaushe ya ha]u da baki, wato lokacin da Larabawa da Turawa suka shigo }asar Hausa. Wannan zuwan na su ya yi tasiri ainun a wajen suturar Hausawa. Domin zuwan na su ya samarwa da Hausawa wasu nau'in suturar da a da ba su da ita. Ga ka]an daga ciki:

1- Gyauto
2- Wando
3- Fatari
4- Zani
5- Rawani
6- Mayafi
7- Riga
8- Taggo
9- Fatala
10-Alkyabba
11-Hirami
12-Tishit.
13-Jeans

**TUFAFIN FULANI**

Fulani kamar yadda aka sani Makiyaya ne. Don haka akasarin tufafinsu }anana ne ba kamar na Hausawa ba. Haka kuma Fulani suna ri}on al'ada matu}a. Dalili kenan ake ganin ba su cika aron al'adun wasu ba}i ba ta fuskar tufafi. [an dama- dama a wannan lokaci yaransu sun ]an ari suturar Turawa, wato }anana riga da jeans. Sakamakon yadda tela yake ba su wahala. Daga cikin tufafin Fulani akwai na maza da na mata kamar haka:

Tufafin Fulani maza manya da yara, Fulani suna sa rigar saki ce mai kama da yar shara wadda aka yi wa ado da ulu a wuya da gaba. Tana da aljihu biyu a gefenta. Sukan kuma

ha]a ta da wando wanda ake kira “ka-haye-ruwa” . Sannan su sa hula ha~ar kada wadda ita ma aka yi wa ado da zaren ulu. Haka kuma suna ya fa gwado a saman rigar sannan su rike sanda, da madubi, wani sa’in da malafa da jallo. Mata kuma suna sa rigar saki ce wadda aka yi wa ado sosai a gabanta da zaren ulu ja da kuma fasasshen madubi. Tsawon rigarsu bai wuce cibiya. Suna ]aura adiko a ka, su kuma ]aura zane da ake kira mudukare. Fulani mata ba su da tufafi da yawa kamar na Hausawa.

Amma a wannan zamani, su Fulani ba su aro kayan wasu daban ba, sai dai kayan Hausawa. Sakamakon zamantakewar da ke tsakaninsu.

## KAMMALAWA

Kamar yadda aka gani cewa, mun ga waye Bahaushe da kuma Bafulatani. Sannan muka ga irin zamantakewar da ke a akwai tsakanin Hausa-fulani da makwabtansu. Bayan haka kuma mun ga irin kallon da na kusa suke yi wa Hausawa da Fulani. Sannan mun ga yadda na nesa ke yi musu. Sannan sai muka duba ainihin suturarsu. Kamar yadda aka sani cewa tun fil azal Hausawa da Fulani suna da tufafinsu na gargajiya, masu }ima da ban sha’awa a idanun sauran }abilun da suke kewaye da su.

## MANAZARTA


Abdullahi, H. (2015) Who are Hausa/Fulani? 1st International Conference Organized by The Department Of Nigeria Languages And Linguistics, Kaduna State University, Kaduna State.

Bunza Aliyu Muhammad, (2015) “A ji Bahaushe, a ga Bahaushe, a san Bahaushe ya yi Bahaushe. (Tsakuren ficen Bahaushe da Tasirinsa a Duniyar {arninsa)” Takardar da aka gabatar a Sashen Nazarin Harsunan Najeriya, Jami’ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato. Domin walimar samun}arin girma ga Dr. Ibrahim Sarkin Sudan Kwantagora. BA, MA, Ph’D, zuwa Associate professor a ~angaren al’adun Hausawa. {ar}ashin jagorancin Farfesa Abdulhamid [antumbishi shugaban Sashen Nazarin Harsunan Najeriya, a babban ]akin taro na PTF Hall ranar laraba, 5 ga Ogusta, 2015 da karfe 10:00am.

Bunza Aliyu Muhammad, (2015) “Matakan Kyallaro Asalin Bahaushe:( Ruwa na }asa sai ga Wanda Bai Tona Ba)” Takardar jagora da aka gabatar a taron }ara wa juna sani na }asa-da-}asa na farko a Jami’r Jihar Kaduna, }ar}ashin inuwar Hausa Studies Scholars Association, kulawar Department of Nigerian Languages and Linguistcs bisa taken ‘The Hausa People, Language and History: Past Present and Future’ Ranar 15-17 Disamba 2014 a Arewa House , Kaduna.

Busa, M. A da Isah, G. (2015) Kalmomin Makwabtan {abilu A Harshen Hausa. 1st International Conference Organized by The Department Of Nigeria Languages And Linguistics, Kaduna State University, Kaduna State.

Funtua, Aliyu Idris; Gusau Sa’idu Muhammad (2010) *Al’adu da ]abi’u Hausawa da Fulani. Eds*

Maigandi Attahiru, (2013) “Fulani da Hausawan gundumar Sakkwato: Bir~ishin dangantaka ta share jini a koma wasa*” [un]aye Vol. 1: Number 6: Journal of Hausa Studies. Department of Nigerian Languages, Usmanu [anfodiyo University, Sokoto.*

Nashayya, B. M da Bisalla, B.A (2015) Who Are The Hausa/Fulani? 1st International Conference Organized by The Department Of Nigeria Languages And Linguistics, Kaduna State University, Kaduna State.